Almabra na dangin manzon Allah da sahabbai
silsila na tarihin dangin manzon Allah da sahabbai

# شذى الياسمين

## في فضائل أمهات المؤمنين

بلغة الهوسا

# Shazi ilyàSIMIN

## Tcikin falalan uwayen muminai

Bugàwa:

**Markazul bahwas wa diràsat**
**Mabra na dangin manzon Allah da sahabbai**

ترجمة: مؤسسة القلم الخيرية العالمية للبحوث والترجمة والتعريب (السودان)

**فهرسة مكتبة الكويت الوطنية**

**Fahwasatu maktabatul kuwet wadniya asnà'a nashri**

Mabratul Àl wal ashàbu - Alkwet

Shazi ilyasimin fi fada ilu ummahàtul muminun

Ta-1 Akwet: Mabratul Àlu wal ashabu, 2005

35 sm. – (silsilata sinul Al wal ashabu)

1- Zaujàtu nabiya.
2- Ummahatul muminin
3- Almuhajiruna wal ansàr

Radmak: 5-0-235-99906

Rakmul idal: 00254/2005

Hakokin bugawa kiayewaga kiawawan ayuka nadangin manzon Allah da sahabbai saidaiga Wanda yake so ya watsa alheri da sharadi kada tcanza darusa na ilmi

**Bugu na Uku**
**1431H-2010M**

**Kiawawan ayyuta na dangin manzon da sahabbai**

Labban wayan hannu: 2560203 – 2552340  fakis: 25603462
S.B: 12421 Shàmiat ramzulbaridi 7165 kuwet
E .mail: almabarrh@ gmail.com
www.almabarrh.net

# Mai fassa da harshen hausa shine dan uwanku a addini (USMAN BN Umar).

بسم الله الرحمن الرحيم

***Da Sùnan Allah mai rahama maijinkai***

"النَّبِيُّ أَوْلَى بِالْمُؤْمِنِينَ مِنْ أَنفُسِهِمْ وَأَزْوَاجُهُ أُمَّهَاتُهُمْ"
(الأحزاب: ٦)

"**Annabi ne mafi cancanta ga muminai bisa ga sukan sù kuma matansa uwayensu ne**"
*(Ahzab: 6)*

## Gabatarwa
## Uwayen muminai a gabàna

Godiya ta tabbata ga allah tsira da aminci su tabbata ga tcikamakin annabawa tare da dangin sa da sahabbansa da wayanda suka bishi har zuwa rana ta karshe kuma bayanhaka:

Hakika yan gidan annabi tsira da aminci su tabbata a gareshi sun sàmu matsayi mai girma da darajia ma daikakio daga farko ziwa karshe gurin ma-abuta sunnah kuma datcewa da hakokin shari-a wanda Allah ya shar-anta a gare su na soyaya da jibinta, wannan kiayewane daga wasiyan manzon Allah «ina tunà muku Allah cikin mutanen gidana»[1], saboda haka ne suke kiaye duk abinda zai cutar da sàshen dangin manzon Allah kuma yasà kinsu.

Musulmai ga baki daya da ma-abuta sunnah a kebe suna son yen gidan manzon Allah màsu tsarki kuma suna haramta cùtar de su ko sàba masu da dukkan wani sabani; ga uwayen muminai kuma cùtarwa kebancece. Kuma nabrah na dangin manzon allah da sahabbai tana so ta gabàtar da cigaban bincike domin ta tabbatar da manufà ta Mabrah na isar da watsa kiawawan ayuka na dangin manzon Allah da sahabbai.

Masu tsarki da sahabbai zabàbu, da tcusa kaunansu cikin zukatan musulmai da fahintar da musulmai daga fahimta na kuskure wayanda suke yi wa sahabbai.

Yayin da wayannan takardu suke kunshe da sha-ani mai g irmà na uwayen muminai da darajojinsu Allah ya kara masu yardà, daga Alkur-ani maigirma da kuma hedisai màsu tsarki tcikin yabon uwayen muminai da kuma nuna daukaka a garesu cikin abin da yake nuna daukakansu, kuma ya daukaka matsayinsu da darajoyinsu gaba daya yana da matsayi kedancece.

[1] Sahihi moushim: kitàbufadà-ilu sahaba, bàbu min fadà-ilu Aliyu BN Abidalib lamba (8042).

**Muhimmin karàtu:**

Allah madaukakin sarkci yàcè: (Annabi ne mafi cancanta ga mumai bisa ga sù kansu kuma màtansa uwayensune) (al-Ahzàb: 6).

Shi mumini: uwayensa màtan annabi[1], kuma bàbansa manzon allah tsirà da aminci su tabbata a gare shi, yan uwan sa sune muhajirai da ansàr ma-ananshi shine addua wanda yake yi (ya ubagiyinnu ka gafarta mana tare da yan uwannu wayanda suka rigamu cikin imàni) (Alhashr: 10).

Wannan shine gidan annabi duk wanda yayi mumunan maganà game da daya daga cikin màtansa to shi baya da imani. Saboda da yana da imani da bazaiyi mumunan magana ba game de (uwayen muminai Saboda da baya batanci game da uwansa.

Kuma wannan zance kamar maganàce ta hakika cikin abinda yake na alfarmà da daukaka da alfahri.

Shin akwai uwaye màsu daukakà daga màtà wanda manzon allah ya zàbèsu? Saidai Allah mai girma da daukakà shine ya zàbèsu. Yace wa anna binsa (wayansu màtà bà su halatta a gareka ba bayan wayannan kuma kada ka tcanza su da wayansu màtan ko da màtan sun yi maka kiawo sai dai abinda hanunka na dama ya mallakà lallai allah mai tsarewàne ga dukka n komai) (al-Ahzàb: 52). Kuma yace game da zainab yar jahshi? (to lokakin da Zaidu ya kàre bukàtarsa daga gare ta, mun aurar dakai ita, domin kada wani kunci ya kasanca a kan mùminai acikin auren màtan diyan han kàkansu, idan sun kàre bukàtà daga garesu kuma umurnin Allah ya kasance abin aikatawa) (al-Ahzàb: 37).

Kuma Allah yace cikin falalansu a kan dukkan matan talikai (yà màtan annabi baku zama kamar kowa ba daga màtà, idan kunyi takawa) (al-Ahzàb: 32). Har Allah ya haramtà wa muminai aurensu kamar yaddaya haramtà wa da auren mahaifiyensa, tare da cewa yin haka halal ne tare da waninsu, sai yace (kuma baya halatta a gareku ku cuci manzon Allah kuma baya halatta ku auri màtansa a bàyansa har abada Lalle wannan a gareku yà kasance babban abu a wurin Allah) (al-Ahzàb: 53).

---

[1] Shi ubàne Saboda fadan annabi : (Lallai ni ina matsayin ubàna) abù dàwad ya ruwaito. Littafin tsarki babin karhancin fiskantan alkibba gurin bàyan geri. Lamba (8) Abbàni ya inganta wannan kadisi.

Duk wanda ya sàbà wa màtan manzo cikin magana ko aiki to hakika ya cùtar da manzo. Zuwa dokan da Allah ya kafà wa muminai cewa kada suyi masu maganà sai bayan shànaki

Sai Allah yacè (kuma idan zàku tambaye su wadansu kàyà, to ku tambaye su daga bàyan shamaki. Wannan yà fi muku tsarki ga Zukatanku da Zukatansu kuma baya halatta a gare ku, ku cùci Manzon Allah) (al-Ahzàb: 53). To mai yasa za mu yi munànan maganà game da su kuma mu zagesu kuma mu danganà su inda bai kumàta ba! Kuma Allah ma daukakin sarki bàyan Ayan da ya gabàtà yana cèwa (yà kai annabi! ka ca wa màtan aurenka da yà'yanka da màtan muminai su kusantar da kasà daga manyan tufafin da ke a kansu. Wancan ya fi sauki ga à ganesu domin kada a cùce su. Kuma allah yà kasance mai gàfara mai jin kai) (al-Ahzàb: 59).

Sa 'annan Allah yace a àya mai biyota (Lalle idan munàfukai da wadanda yake akwai wata cùta a cikin zukàtansu, da màsu tsègumi, a cikin madina, ba su hanu ba daga hàlàyensu Lalle, zà mu shùshuta ka a garesu, sa'annan bà zà su yi makwabtakà da kai ba, a cikinta, fàce kadan) (al-Ahzàb: 60). nùni gawadanda suke dangana wannan ga màtan annabi tsira da aminci sutabbata a gareshi. Kuma wannan ya kasance ga màtan da zaidu ya rabu da ita bayàni ya wuce a cikin ta (37). Sai ya sanya maganganu ga munàfukai da ire irensu dangane da màtan manzon Allah. Kuma ina yiwa muminai wasiya kada su kasance kamar wayannan munàfukai.

Kuma Allah yayi bayanin cewa bàzai karbi uzuri ba baga wanda yayi mumunen maganà dangane da màtan manzon Allah. Saboda yà bar Alkur ani da sunnah kuma yà bi maganan màsu girman kai idan bai tuba ba kuma ya mutu a cikin wannan-kuma yadda yace (ranar da ake juya fuskokinsu a cikin wuta, sunà cèwa, kaitonmu, saboda rashin biyaryanmu ga Allah da rashin biyaryanmu ga manzo « 66 » kuma suka ce ya ubangijin mu lalle mù munbi shugabannin mu da manzon mu! sai suka batar da mu daga hanya) (al-Ahzàb: 66-67).

Kuma shin mumunan magana game da màtan annabi wanda bai cancancesu ba maganane mai kiawo? Ko kuma yana daga cikin abin ki mai tsanani? Ka dauki kanka ga ka ga manzon Allah, kanà zàgin Aisha ko Hafsat Wani irin kollo manzon Allah zai yi maka? Kuma yàyà manzon Allah zai daukeka?!

## Màtan annabi tsira da amincin Allah su tabbata Agareshi mafifitan màtan talikai

Saboda fadan Allah ma daukakin sarki (yà matan annabi ! baku zama kamar kowa ba daga màtà idan kun yi takawa) (al-Ahzàb: 32). Wato bàbu wayansu màta wayanda suka kaisu daraja, da sharadin takwa. Idan takawa ya tabbata cikin hakinsu to fifiko ya kedantce wayansu a cikinsu ba, kuma Allah madaukakin sarki shine ya zabesu tàre da manzon sa tsira da aminci su tabbata a gareshi!

Amma jin tsoron Allah tabbatatce ne ga matan manzon Allah cikin nassin littafi mai girma, Saboda sun zàbi Allah da manzon su da gida na làhira akan ràyuwan duniya da kawanta, bayan saukan àyà na bàsu zàbi ita tce: (yà kai annabi ! ka ce wa màtanka, idan kun kasance kunà nufin rayuwar dùniya da kawarta, to, ku zo in yi muku kyautar ban kwàna, kuma in sake ku, saki mai kyau. (28) kuma idan kun kasance kunà nufin Allah da manzonsa da gidan làhira, to Lalle, Allah yà yi tattalin wani sakanako mai girma ga màsu kyautatàwa daga gare ku) (al-Ahzàb: 28 - 29). Sai suka zàbi Allah da manzon sa da gidà na làhira, Suka bar yà kasance gaskiya sabida, sun rayu da manzon Allah ba tàre da son abin duniya ba ;wannan ya kasance abin da ya gaskata imàninsu da hakikanin jin tsoron Allah.

Kuma Lallai wannan zàbi tsayayene akan jin tsoron Allah shi yasa ya tcantcantci karbuwa a wurin Allah sai ya daukakà su ta dalilin wannan. Kuma saboda fadinsa ma daukakin sarki: (wadansu màtà bàsu halatta a gare ka a bayan haka, kuma ba zàka musanyasu da màtan aure ba, kuma ko kyaunsu yà bàka sha’awa, fàce dai abin da hannnun dàmanka ya mallaka. Kuma Allah yà kasance mai tsaro ga dukan koma) (al-Ahzàb: 52)

**Kuma wannan girmamawa ta bangare buyu ne :**

1. hana manzon Allah kàra màtan aure akansu

2. hana manzon Allah yasaki daya daga tcikinsu domin ya auro wata.

Saboda haka ne zasu kasantce màtan sa na kowane lokaci bawai a nan duniya kowai ba har lahirah shi yasa: ya hana muninai auransu koda bayan ranshi, Allah ma daukaki ya ce: (kuma bàyà halatta a gareku, ku

cùci manzon Allah, kuma bà ya halatta ku auri màtansa a bàyansa har abada. Lalle wannan a gare ku yà kasance babban abu a wurin Allah) (al-Ahzàb: 53), kuma ya sanya suku zama matsayin uwayen muninai a inda yatce: (annabi mafi cancanta ga miminai bisa ga kansu, kuma màtansa uwàyen su ne. Kuma ma'abùta zumunta wadansun su sun fi wadansu a cikin littafin Allah bisa ga muminai da muminai da muhàjirai, face fa idan kun aikata wani alheri Zuwa ga majibintanku, wancan yà kasance a cikin littafi, rubutacce) (al-Ahzàb: 6).

Wayannan ayoyi sun isa abin dubawa ga me hankali, cikin girman sha' anin uwayen muminai Allah ya kàra masu yardà.

## Hikiman adadin màtan annabi

Yayinda rayuwan annabi ya kasance abin koyi ga muminai kamar yadda yake a cikin lattafi mai girma (Lalle abin koyi mai kyau ya kasance gare ku daga manzon Allah ga wanda ya kasance yana fàtan rahamar Allah da ramar lahira, kuma ya ambaci Allah da yawa) (al-Ahzàb: 12). Kuma ayukan manzon Allah sun kasance mafarin duk wani aiki na Shari-a.

* ya kasance babu makawa daga sàmun wanda zai dauka daga cikin gidan annabi mai tsarki, kuma wannan yana daga hikiman adadin matan aure dangane ga annabi, domin mu dauki hukuntce hukuntce, dana aurataya da hukuntci kebantcace ga muminai màtà cikin zamaninsu, Allah yakara masu yarda dakuma bayan zàmaninsu zuwa rànan kiyàma.

* Kamar yadda suka samu tarbiya gurin annabi Yana da kiawo ga mata muminai suyi koyi da su cikin duka ayyuka.

* Kuma ya isa godiya ga Allah cikin wannan baiwa Wanda yayi masu sune abin koyi mai kiawu ga dukkan màta muminai.
Kuma wannan ya kasance hikiman adadinsu. Ga daya daga cikinsu itace shugabanmu Aisha Allah ya Kara mata yarda, tana daga cikin wayanda suka fi ruwaito hadisan manzon Allah.

* Yayin da muslunci ya kasance a zamaninsa babuu makawa sai an isar da shi cikin kabilu da gurbatattun larabawa, domin saukaka kira cikin musulunci. Kamar aurensa da zuwairiyatu Allah ya Kara mata yarda. Yà kasance dalilin da ya saka kabilar bani mudalik suka musulunta.

* Kuma ya kasance kari gurin sadar da zumunci ga sahabbansa masu girma da kuma girmamasu da daukakasu, kaman abubakar da umar Allah, ya kara masu yarda, hakika ya auri yayansu Aisha da hafsat allah ya kara masu yarda, kamar yadda ya daukaka usman da Aliyu da auren yayansu Allah ya kara masu yarda gaba daya.

* Haka kuma auren wayansu daga cikinsu ya kasance dalilin tabbatar da hukuncin shari'a kaman bata hukuncin tabanni, kuma wannan ya tabbata ne yayin da manzon Allah ya auri shugaba zainab yar jahshi Allah ya kara mata yarda.

Haka kuma ga sashen wayansu màtan annabi kamar saudatu yar zam-atu Allah ya kara mata yarda wanda mijinta ya rasu, da shugaba ummu habiba yayinda mijinta yayi rida ya fita musulunci a garin habasha sai ta saura cikin darul-gurba, kuma wannan ya kasance garabasa ga wayannan màtan annabi.

Yayin da ya tabbatà game da daya daga cikin màtan annabi tcewa ta girmeshi da shekara goma sha biyar, shi kuma yana cikin samartakan sa, sai dai sauran màtan sun kasance yan mata masu kananan shekaru, sai dai ya kasance akwai budurwa guda daga acikinsu itace nana Aisha sauransu daga sakaku sai zaurawa wa yanda mazajensu suka mutu wannan ya nisanta ga dukkan nisanta gurin za be da sha'awa.

## Rayuwa gaba ki daya uwayen muminai

Duka matan manzon Allah wayanda ya zauna tare da su har ya rasu ya barsu, fatce khadija da zainab yar huzaima Allah ya kara mata yarda- hakika wayannan su biyu sun rasu manzon Allah yana rayè.

- Kuma dukaninsu an binne su a makabartan baki'a na madina banda khadija ita an binneta a hajun a cikin garin makkah, da maimuna ita an binata a sarfi kusa daga tan-im gurinda manzon Allah yayi gini, goma daga cikin màtan manzon Allah sun hadu tare da shi gurin dangantaka ta bangaren uba: ummu habiba, khadija, Aisha, hafsa, sauda, zainab yar jahshi, juwairiya, zainab yar khuzaima, maimunatu, ummu salama, kuma ya hada uwa da uba, uwanta itace aminatu yar abdul-mudalib gogon manzon Allah, sun hadu kuma ta bangaren uba gurin khuzaimatu dan madrakatu dan ilyasu.

Annabi tsira da aminci su tabbata a gareshi ya sanya sunan màtansa biyu maimuna da juwairiya bayan sun kasance ba sunaye masu kuawu ba.

- Ya kasance daga zainab yar khuzaima da safiyat da maimuna da

- Da khadija allah ya kara masu yarda hakika sun auri mazaje biyu kafin su auri annabi yayin da aisha ita ka dai ta kasance budurwa a cikinsu, (Allah yak ara masu yarda).

## Falaloli baki daya na uwayen muminai

1. Su màtan manzon Allah ne aduniya da lahira. Tsarkake yan gidan manzon Allah daga kazanta (shirka da shaidan da ayyuka mara kiawu da halaye mara kiawu), da uwayen muminai daga yan gidan manzon Allah, Allah ma daukakin sarki ya ce (ya màtan annabi baku zama kamar kowa ba daga mata idan kun yi takawa, saboda haka, kada ku sassautar da magana, har wanda ka da cuta a cikin zuciyarsa yayi dammani, kuma ku fadi magana ta alheri. (32) kuma ku tabbata a cikin gidàjenku, kuma kada ku yi fitar gàye gàye ta jàhiliyyar farko. Kuma ku tsai da salla, kuma ku bàyar da zakka, ku yi dà 'a ga Allah da manzon sa.Allah na mufin ya ta fiyar da kazanta kawai daga gare ku ya mutanen babban gida: kuma ya tsarkake ku, tsarkakewa. (33) kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin dàkunanku daga ayoyin Allah da hukunci.Lalle Allah ya kasance mai tausàsawa, mai labartawa. (34) (al-Ahzàb: 32 - 34), àyoyi suna bayyana mana tcewa tsarki ya taru ga màtan sa ne tsira da aminci su tabbata a gareshi, yaya à-a kuma hakika ya sauka a kansu ne.
2. Matsayi na daban saboda muminai yayin da Allah ya sanya suka zama uwayen muminai cikin haramci da alfarma falala daga sahabbansa tsira da aminci su tabbata a gareshi.

   (Annabi ne mafi cancanta ga muminai ga su kansu, kuma matansa uwayensu ne) (al-Ahzàb: 6).
3. Sun zàbi Allah da manzonsa dagida na karshe kuma sun daukaka su akan duniya da abin adonta, wannan ya kasance sakama konsu lallai Allah yà dànadar madsu da sakamako mai girma.

   (Yàkai annabi! ka ce wa màtanka, idan kun kasance kuma nufin rayuwar dùniya da kawarta, to ku zo in yi muku kyautar bankwàna, kuma in sake ku, saki mai kyau (28) kuma idan kun kasance kunà nufin Allah da manzonsa da gidan lahira, to, lalle Allah yayi tattalin wani sakamako mai gir ma ga masu kyautatawa daga gareku) (al-Ahzàb: 28 - 29).

   Kuma sananene tcewa sun zabi Allah da manzonsa, shi yasa manzon Allah bai rabu da su ba.
4. Ninkin làlà wanda suka da shi idan suka yi biyaya da kuma aiki ma kyau: (kuma wadda ta yi tawati'u daga cikinku ga Allah da manzon

sa, kuma ta aikata aiki na kwarai, za mu bata sakamakonta ninki biyu, kuma mun yi mata tattali, na arziki na karamci) (al-Ahzàb: 31)

5. Uwayen muminai ba su zama kamar kowa ba daga màtà gurin daukaka da falala da darajà: (yà màtan annabi! baku zama kamar kowa ba daga màtà, idan kun yi takawa, saboda haka kada ku sassautar da magana, har wanda ke da cùta a cikin zuciyarsa yayi dammani, kuma ku fadi magana ta alheri) (al-Ahzàb: 32).
6. Daukaka wanda allah yayi masu na karatun alkur-àmi da kuma hikmaa cikin gidàjensu, yana nùna kuduran su da kuma daukaka.

   (Ku tuna abinda ake karantàwa a cikin dàkunanku daga ayiyin allah da hukunci lalle allah ya kasance mai tausayàwa mai làbartàwa) (al-Ahzàb: 34).

## Falalà kèbancece na kowane daya daga cikinsu

### 1) Uwar muminai Khadija yar Khuwailid Allah kara mata yarda:

Itace khadija yar khuwailid dan asadu dan abdul aziyu dan kusai kàkan annabi tsira da aminci su tabbata a gareshi, itace na biyu mafi kusantci gurin dagantaka da manzon Allah, daga cikin màtansa, ta bangaren uba, kuma bayanta bai auri wata màta ba daga zuriyan kusayi sai ummu habiba yar abu sufyàn.[1]

Kuma khadija tana daga cikin màtan kuraishàwa, ma daukaka, kuma mafi daukakansu, kuma ta fi su dukiyà, manzon Allah ya aureta yanà shekarà ashirin da biyar bayan tà taba auren abi hala dan nabash dan zararatu tamimi halifa dangin abdu-dàr.

Manzon Allah ya aminta da ita kuma ta taimakeshi, yà kasance yanà fifitata akan dukkan màtà,[2], itace ta haifa masa yayansa, se dai ibrahim kawai shi sayada maria itace ta haifeshi, manzon Allah bai auri wata ba har sai Lokatcin da ta rasu bayan shekara uku daga hiyra

### Daga cikin matsayin ta, Allah yak ara mata yarda:

1. tana daga cikin wayanda suka fara shiga musulunci: ita ce farkon wanda ta fara mafarki da abin da Allah ya saukar, ta nà da lada làdan wayanda suka yi imàni a bayanta.[3]

---

[1] Ummu habibi ta hada dangantaka da manson allah gurin kàkà abdu manàf dan kusai ita kuma khadija ta hada dangantaka da manson Allah gurin kàkà kusai, amma sauran màtan manzon Allah sun hada dangantaka dashi ta wayansu bangare « muratu, da ka – abu da la –aya, da khuzaimatu, da ilyàsu da midra».

[2] Wato akan dukkan màtan tcikin zamaninta, tana daga tcikin manyan matan talikai guda hadu, sune asiyatu yar mazàhimu màtan fir-auna, da maryan yar imran, da khadija, da fàdimatu allah ya kàrà masu yarda baki dàya.

[3] Saboda itace farkon matce wanda ta fara shiga musulunci kuma wanda ya fara kawo aiki mai kiawu yana da ladan aikin, kuma yana da ladan wanda ya aikata irin wannan aikin, kuma mai nuni ga aikin alkhairi kamar wanda ya aikata yake cikin lada, kuma wanda yayi kira zuwa ga shiriya yana lada irin na wayanda suka bishi, wannan ladan ba zai rage kamai daga ladan su ba. Kadùba fasaran wannan mas-ala a cikin : fathul bàri « babin falalan khadija », kuma ka dùba cikin: nihayatu ijazu fi siratu sakinul hijàzu, na dahdàwi, kuma da sharhu nawawi na sahihu muslin.

2. Manzon allah be auri wata mata ba har sai lokacin da ta bar duniya ta zauna shekara ashirin da biyar daga shekara talatin da takwas itace rayuwar aure na manzon allah «kusa da sulusi biyu».
3. So wanda ta keyi wa manzon Allah ya kasance arziki agareta daga Allah kuma arziki agareshi son da takeyi masa falalane.[1]
4. Manzon Allah ya kasance yana yawaita ambaton ta yana daukakata yana yabonta kuma yana nuna misàli da ita.

   Har nana Aisha Allah ya kara mata yarda ta tce «menene ya dauke hankakin manzon Allah zuwa kan khadija fiye da yanda yake tunànin sauran matansa,saboda yawan ambatonta wanda yaka yi kuma ni ban taba ganinta ba».[2]
5. Ta kasance mafificia cikin ga màtan al-umman muhamad tsira da aminci su tabbata a gareshi.

   Bukhari yà rawaito da isnadinsa ga Aliyu dan abi dàlib Allah yakara masa yardà ya ce: na ji manzon Allah tsira da amintci su tabbata a gareshi yana tcewa: «mafi alkhairin matan ta maryam kuma mafi alkhairin màtan ta khadija».[3]
6. Amincin Allah ya tabbata agareta kuma bishara agareta da gida cikin aljannà daga aiki ba rashin aiki a ciki kuma ba dangantaka.

   Bukhàri da muslin sun ruwaito da isnadinsu zuwa ga abi huraira Allah ya kàna masa yardà ya tce: « mala-ika jibril ya zo gurin annabi tsira da aminci su tabbata a gareshi sai ya tce: ya manzon Allah wannan khadija ce hakika ta zo gurinka ka yi mata sallama daga ubangijin ta kuma daga gereni kuma kayi mata bishara da gida a cikin aljanna daga aiki ba rashin aiki a ciki kuma babu dangantakà».[4]

---

[1] Sahihu muslim: kitabu fadà-ilu sahàba, bàbu min fada-ili khadija lamba (5342), kuma a cikin hadisi: «manzon Allah yace Lalle hakika na azirta da son ta» sai ka duba yaya son ta ya kasance arziki daga Allah zuwa ga manzon Allah tsira da amintci su tabbata a gareshi.

[2] Sihihu muslim, kitàbu fada-ilu sahaba, bàbu min fadà-il khadija lamba (5342)

[3] Sahihul bukhari: kilabu fada-ilu sahàba, bàbu tazwiju nabiyu khadija wa fadliha lamba (3815)

[4] Sahihul bukhaàri: kitabu fada-ilu sahàba, babu tazwiju nabiya khadija wa fadliha lamba (3820)

7. Allah yà azurtàshi da yaya daga gareta wanda a gareshi yà tce «Allah ya azurtani da yaya daga gareta wanda bai azurta mini daga wata ba».[1]

**2) Uwar mumunai Saudatu yar Zam-atu Allah ya kara mata yarda:**

Itace saudatu yar zam-atu dan kaisu dan abdu shamsu dan abdu wuddi dan nasru dan màlik dan hislu dan Amir dan la-ayu dan gàlibu dan fahru, mahaifiyarta itace Ashamùsu yar zaidu dan Amri Al-Ansàriya, tà kasance kàfin annabcin annabi tsira ta aminci su tabbata a gareshi tana gurin abdu kasranu dan amri, ta ruwaito daga annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi kuma daga gareta akwai BN abbas da yahyà dan abdullahi dan abdur-rahman zararatu, ta shiga musulunci a garin makkah da dadèwa kuma tayi hijra tare da mijinta zuwa habasha hijrah ta biyu,mijin ta ya rasu a hurin hijrah, abdu kasrànu dan amri, ta ruwaito daga annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi kuma daga gareta akwai BN Abbas da yahyà dan abdullahi abdur- rahman dan sa'-adu dan zaràratu, ta shiga musulunci a garin makkah da dadèwa kuma tayi hijrah,[2] kuma itace farkon màta wanda manzon Allah ya aura bayan khadija kuma wannan ya kasance a garin makkah, kumata zauma tare da shi misatin shekara hudù, itace sayidatu jalilatu da mabilatu ta resu a lokacin karhen sabànin umar dan khadàb.

**kuma daga cikin matsayin ta, Allah yakara mata yarda:**

1. Kuadayinnta na wanzuwa a gidan annabi tsira da aminci su tabbata a gareshi, hakika wata rànà tayi wa Aisha rantsuwa saboda son kusanci ga manzon Allah da kuma soyaya a gareshi, kuma ta kasance tcikin màtan annabi na cikin aljanna.

   Ibnu mas'ùdu ya kawo cikin dabkàt lallai saudatu tà tce wa annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi: ina neman taimako a gurinka domin Allah, ka mayar da ni hakika na tsùfa bana bukatan namiji se dai ni ina so a tasheni rànar alkiyàna tcikin màtan ka, sai manzon Allah ya aure ta.[3]

---

[1] Rawawu dabràni fil mu-ujimul kabir, lamba (22) bàbu zikru azwaju rasùlul-lahi wa hunna khadija bintu khuwailid j (23) s (13).

[2] Tahzibu tahzibu, BN hajar Al-askalàni, (12/455).

[3] Bitasarifu min dabkàt Bn sa'ad ( 8/45).

Bukkari ya ruwaito da isnà dinshi gurin Aisha Allah ya kàra mata yardà: «Lallai saudatu yar zam'atu ta sàmu rànanta a gurin Aisha annabi ya kasance yana yi wa Aisha rantsuwa da rànanta kuma da rànan saudatu».[1]

2. 1-Aisha tanà bùrin ta kasance tanà da irin kautar ta da kuma hanyan ta.Muslin ya rawaito da isnadinshi ga Aisha Allah ya kara mata yardà tà tce «ban ga wata màtà wanda na so na kasance kamar ta ba,[2] Kamar saudatu yar zam'atu..».[3]

### 3) Uwar uminai Aisha yar abi Bakar Sidik Allah yakara mata yarda:

Itace Aisha yar abibakar sidik kuma shina abdullahi dan usman taimiyu kurshiya ana yi mata kinaya da ummi abdullahi, hakika ta tambayi manzon Allah yayi mata kinaya, sai manzon Allah ya ce: zanyi miki kinàya da dan yar uwanki, sai ya yi mata kinàya da ummi abdullahi, shine Abdullahi dan zubair dan awan kuma Asmàu yar abibakar Allah ya kara masu yarda, kuma mahaifiyarta ummu rauman yar uwaimir Alkinaniya, an haifeta bayan annabci da shekara hudu, manzon Allah yà aurèta tana shekara shida kuma ya tare da ita tana shekara tara, kuma bai auri wata budurwa ba sai ita, kuma ta kasance mafi soyuwa gurin manzon Allah daga màtan sa bayan khadija, kuma mace mafi ilimi cikin màtan al-umman annabi Muhamad, Manyan sahabbai sun duaki fatwà a gurin ta.[4]

Tarasu gurin manzon Allah tsira da aminci sa tabbata a gareshi tana shekara ashirin da takwas kuma rasuanta ya kasance cikin 17 ga watan ramadan shekara 58H, Abù huraira Allah, ya kara masa yardà shine yayi mata sallah kuma aka binneta a makabartan baki'a.

### Kuma daga cikin matsayin ta'allah ya kara mata yarda:

1- Ta kasance mafi soyuwa gurin manzon allah daga màtansa bayan khadija.

---

[1] Sahihu bukhari : kitàbu nikàhi, bàbulmar'atu tahbu yauniha min zaujiha lidura tiha lamba (5212).

[2] Sahihu muslim : kitàbu nikàhi, bàbu jawàzu habatiha nawbatiha liduratiha lamba (1463).

[3] Fi mislà khiha bikasri awalili ay jildiha, abin nufi shine takasance kamar ita a cikin komai.

[4] Ràjia-nutafadilan li-iradu mastadrakathu Aisha Ala sahàba na badni din azarkashi.

Bukhari ya rawaito da isnàdin daga amri da àsi Allah kàra masa yarda « Lalla annabi tsira da aminci su tabbata agareshi ya aikeshi zuwa ga runduna mai yawa ya tse : sai na zo gurinshi sai na tce wayanna mutàne ne sukafi soyuwa a gareka ? Sai ya tce Aisha, sai na tce a cikin mazà fa ? ya tce mahai finta..»[1]

2- Mala ika jibril ya zo wa manzon Allah da hoton ta a cikin wani gutsure na hariri kafin ya aureta.

Bukhari da muslim sun ruwaito da isnàdinsu zuwa ga Aisha Allah yak ara mata yarda tà tce: manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi yà tce «na ganki cikin mafarki dare uku Mala'ika ya zo mini da ke tcikin yankin hariri yana cewa : wannan màtarkace, sai na yàyefiskanki sai na ga kèce, sai na ce idan wannan yà kasance daga Allah yayi kiawu».[2]

3- Malaika jibril ya aikata tare da manzon Allah tsira da aminci su tabbata a gareshi.

Bukhari ya rawaito da isnàdinsa ga Aisha «ta tce: manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi wata ràna ya tce: yake Aisha, wannan mala'ika jibril ne yane yi miki sallama» sai na tce amincin Allah da rahamansa da albarkan sa su tabbata a gareshi, kana ganin abin da bana gàni-tanà nufin manzon Allah tsirà da aminci su tabbatà a gareshi.[3]

4- An saukar da wahyi ga annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi a cikin dàkinlà banda waninta daga cikin uwayen muminai.

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi yà tce: « … yake ummu sal ma kada ki tcutar da ni game da Aisha; saboda ma rantsa da Allah wahayi bai taba saùka a gare ni ba cikin dàkin daya daga cikin ku, sedai ita»[4]

5- Farkon wanda manzon Allah ya fara ba ta zàbi yayin da Allah ya saukar da àyan zàbi, shina fadansa madaukakin sarki: (yak ai wannan annabi ka yaya wa màtan ka idan kun kasance kuna son ràyuwan

---

[1] Sahihil bukhari : kitabul mugàzi, babu gazwatu zàta salàsil, lamba ( 4358).

[2] Sahihi muslim :kitabu fada ilu sahàba, babu fada'ilu Aisha ummul muminun lamba (2438).

[3] Sahihil bukhari fada'ilu ashàbu, babu fada'ilu Aisha, lamba (8673).

[4] Sahihil bukhari: kitabu fada'ilu as'hàbu nabiyu, babu fadlu Aisha, lamba (3775).

duniyà da kawàce kawàcen ta taku daukakàsu zan jiyar da ku dàku dàdinta kuma na sake ku saki mai kiwu (28) kuma idan kun kasance kuna son Allah da manzon sa da gidà na karshe, to Lalle allah yayi tanadin sakamako mai girma ya wayanda suka kautata a cikin ku) (al-Ahzàb: 28 - 29) kuma wannan ya tabbata da dàcewan iyayenta sai tazàbi mmanzon Allah kafin ta yi muni da su, sai sauran uwayen muminai suka bi hanyan ta.

Bukhari da muslim sun rawaito da isnàdinsu ya Aisha tà tce: «ta wani hanya zan bi umurnin iyayena? Lalle ina son Allah da manzon sa da gidà na karshe, ta tce: sai sauran màtan manzon Allah suku aikatà kamar yadda ta aikatà»[1]

6- àyan alkur'ani ya sauka ta dalinta kuma da abin daya shàfi al'ummà baki daya, da kuma abinda ya kabantce ta:

* Allah ya shaida baranta a gareta daga abin da jefe ta da shi nakirkira karyà da mumunan aiki a daura mata.

(Lalle ne, wayanda suka zo da kiron karyà wadansu jama' na daga gare ku kada ku yi zatonsa sharri ne a gareku. Kowane mutun daga gare su na da sakamakon abin da ya sanà anta na zunubi, kuma wanda ya jibinci girmansa daga garesu, yanà da azabà mai girma) har zuwa fadan sa madaukakin sarki: (miyàgun màta domin miyagun maza suke, kuma miyàgun maza domin miyagun màta suke, kuma tsarkàkan màtà domin tsarkàkan muzà suke, kuma tsarkàkan maza domin tsarkakan màtà suke. Wadannan sù ne wadanda ake barrantawa daga abin da (masukazafii) suka fadà.Kuma sunà da gàfara da arziki nz karanci) (annur: 26).

*Kuma wanda dalili, ta kuma ya shafi al umman musmlmai:*

* Ayan taimamà wanda ta kasance rahma da saukakàwà ga d'umman musulmi bukhara da muslin sun rawaito cikin isnadinsu ga Aisha «tà kar bi wani abin anfani a gurin asmà'a sai ya bata, sai manzon Allah ya aiki mutane daga cikin sahaban sa suje su memo sai sallah ya samesu suka yi sallah babu alwalà. Yayin da suka dawo gurin manzon Allah sai suka bay yanà ma sa abin da ga jàru, sai àyan taimamà ta sauko, usaidu dan hadir ya tce: aiki mutanc.

[1] Sahihil bukhari: kitàbu tafsir, bàbu kauluhu: (wa inkuntunna turidna-làha wa rasù lahu wa dàral àkhirata fa inna làha a'adda lilmuhsinàti minkunna ajran azimà) ( Al-ahzàb :29) lamba (4786).

Allah ya sàkà miki da alkheri me rantse da Allah, wani abin kuntci bai sauka gareki ba fatce sai Allah ya saya maki mafita, kuma Allah ya sanya allarka a ciki ga musulma»[1]

7- Manzon Allah yana kuadayin ya dinga tafiyà a cikin dàkintas kuma an binne shi acikin dàkinta.

8- Manzon Allah ya bayar da labai tcewa tana daga ikin mutanen aljannà bukhari ya rawaito da isnadin shi ga kasin dan muhamad "Lalle aisha tanà kùkà sai ibnu abbas ya zo sai ya tce: yake uwar muminai, garkiyan ki yà rigà yà gaba gurin manzon Allah da abi bakak",[2] ibnu abbas ya yanki mata tcewa shiga aljanna da dàtcèwà.

Kamar yadda tirmizi ya ruwaito kuma ya ingantà daga abdullahi dan zayàdu Al'asadi ya tce «nà ji Ammar yana tcewà: ita màtar sa tce a duniya da lahirà.»[3]

9- Ita tce mafi ilimin màtan wannan al'umma, saboda ta rawaito hadisai masu yawà gurin manzon Allah wayanda sukai dubu biyu[4], kuma bugu dakari manyan sahabbai suna zuwa gurinta su naimi fatawà.

## 4) Uwar muminai Hafsatu yar Umar dan Khadàb Allah kara mata yardà:

Itace hafsatu yar umar dan khadàb, ita yar uwar abdullahi ce saboda mahaifinsa, kuma mahaifiyarta ita ca zainab yar maz'un yar uwan usman dan maz'um dan habibu dan wahbin dan huzàfatu, manzon Allah ya aureta cikin shekara na uku daga hijrà bayan mijintà hanisu dan huzàfatu Albadri wanda ya matu a madina, kunata kasance mai yawan azumi kuma mai yawan tsayuwan dare, an haifeta kafin annabci da shakara biyar kuma tarasu akin watan sha'aban shakara 45H allah ya k0r0 mata yarda.

## Kuma da cikin matsay inta, Allah ya kàrà mata yardà:

---

[1] Sahihil bakhari : kitabu fada'ilu as'hàbu nabiyu, babu fadlu aisha lamba (3773).

[2] Sahihil bukhari: kitabu fada'ilu as'habu nabiyu babu fadà'ilu Aisha lamba (3771).

[3] bukhari ne ya rawaito hitabu fada'ilu sahaba nabiyu babu fada'ilu Aisha lamba (3772), da jàniu tirmizi babu min fada'ilu Aisha, lamba (3889), tirmizi ya tce wannan hadisi mai kiwune ingantatce.

[4] Sayidatu Aisha ta rawaito daga hadisai (2210) ita ce na hudu cikin masu rawaito hadisai bayan abihuraira da abdullahi dan umar da annas dan màlik Allah yak ara masu yardà ka duba: sunayen sahabbai masu ruwaya, na ibnu hazam s (39) da talkihu fuhùmu asar ibnu jauzi s (363)

(1) Ta daukaka saboda tayi hijrà tare da mijinta, ibnu sa'ad ya ruwaito da isnadinsa ga abi huwairis ya tce: (hanisu dan huzàfatu[1] ya aure ta daga hafsatu yar umar ta kasance a wurinshi kima ta yi hijra tare da shi zuwa madina.)[2]

